**GOD'S SIMPLE PLAN OF SALVATION FROM YAHAYA**



# 1. Ba zamu iya ceton kanmu ba."

Yahaya 3:19   Hukuncin kuwa shi ne, haske ya shigo duniya, amma mutane suka fi ƙaunar duhu da hasken, don ayyukansu mugaye ne.



# 2. Mun cancanci mutuwa da jahannama.

Yahaya 6:40   Gama nufin Ubana, shi ne duk wanda yake duban Ɗan, yake kuma gaskatawa da shi, yǎ sami rai madawwani, ni kuma zan tashe shi a ranar ƙarshe."

Yahaya 3:18   Duk wanda ya gaskata da shi, ba za a yi masa hukunci ba. Wanda kuwa bai ba da gaskiya ba, an riga an yi masa hukunci, domin bai gaskata da sunan makaɗaicin Ɗan Allah ba.

Yahaya 3:36   "Wanda ya gaskata da Ɗan, yana da rai madawwami. Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi."



# 3. Jesus was in the world and he died for us.

Yahaya 14:6 Yesu ya ce masa, “Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina.

Yahaya 3:17 Gama Allah bai aiko Ɗansa duniya domin yă yanke mata hukunci ba, sai dai domin duniya ta sami ceto ta wurinsa.

Yahaya 1:10,12 Dā yana duniyar ma ta wurinsa ta kasance, duk da haka duniya ba ta san shi ba. Amma duk iyakar waɗanda suka karɓe shi, wato, masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah,



**Christ died for sinners!**

# 4. Ba zamu iya ceton kanmu ba.

Actes 4:12 Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyar nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto.”

Afisawa 2: 8-9   Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda da aikin lada ba, kada wani ya yi fariya.

Tite 3:5   sai ya cece mu, ba don wani aikin adalci da mu muka yi ba, a'a, sai dai domin jinƙan nan nasa, albarkacin wankan nan na sāke haihuwa, da kuma sabuntawar nan ta Ruhu Mai Tsarki,




# 5.   Saboda mutuwar Yesu a madadinmu, duk abin da ya kamata muyi shine bangaskiya cikinsa, muna amincewa da mutuwarsa a matsayin biya don zunubanmu – kuma zamu sami ceto!

Yahaya 5:24   Lalle hakika, ina gaya muku, duk mai jin maganata, yake kuma gaskata wanda ya aiko ni, yana da rai madawwami. Ba za a yi masa hukunci ba, domin ya riga ya tsere wa mutuwa, ya kai ga rai.

Yahaya 6:47   Lalle hakika ina gaya muku, wanda ya ba da gaskiya, yana da rai madawwami.

Yahaya 10:28   Ina ba su rai madawwami, ba kuwa za su hallaka ba har abada, ba kuma mai ƙwace su daga hannuna.

*Idan kana son ka karɓi Yesu Kiristi a matsayin mai cetonka, ga samfurin addu'a anan. Ka tuna, faɗar wace nan addu'a ko wata addu'a dabam ba zai cece ka ba. Amincewa ce kaɗai cikin Kiristi wanda zai iya cece ka daga zunubi. Wace nan addu'a, hanya ce mai sauƙi a furta ga Allah bangaskiyarka a cikin Sa kuma ka gode masa don ya tanadar maka da ceto.*

**"Allah,**

**na sani cewa nayi zunubi gareka kuma na cancanci hukunci. Amma Yesu Kiristi ya ɗauki hukuncin da ya cancance ni, don ta wurin bangaskiya a cikinsa in sami gafartawa. Na juyo daga zunubaina kuma na sa amincewa tawa a cikinka don ceto. Na gode maka don alherinka mai ban mamaki da kuma gafara – kyautar rai madawwami! Amin!"**

**Amazing Grace Publishing * PO Box 1963 * Joshua TX 76058 * 817-426-1828 * E-Mail JamesAV@aol.com**